رئاسة الشؤون الدينية بالمسجد الحرام والمسجد النبوي

# Hanyoyi masu anfani don samun rayuwa mai dadi

HAUSA

هوســـا

الوسائل المفيدة للحياة السعيدة

Wallafar Shiekh
Abdurrahman Bn Nasir Al-Si'idi
Allah Ya yi masa rahama

# Hanyoyi masu anfani don samun rayuwa mai dadi

**Wallafar Shiekh Abdurrahman Bn Nasir Al-Si'idi Allah Ya yi masa rahama**

## Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

## Takaitaccen tarihin mawallafin wannan littafin

Wannan littafin da yake a gabanmu yana sanya mana wasu hanyoyi na fili don samar da tabbataccen jin dadi na hakika wanda mutum yake lalube da zai yi tafiya mai nisa akansu wadda take nesa da karkacewar Dan Adam wacce ta dogara wajen tsara hanyoyi da kusurwoyi akan dalilai da suke da tushe daga Al'qur'ani mai girma da kuma shiryarwa daga Annabi mai hikima. kuma ita din...A karan kanta ita ce jin dadi da mutum mumini yake burin samunta ,kuma al'umma mumina zata rayu; saboda ita kadai ce hanya kwara daya da zata iya tsara masa rayuwar sa bisa tsoron Allah da kuma yardar sa. Marubucin wannan littafi shi ne: Babban Malamin nan: (Shaikh Abdurrahman Bn Nasir Bn Abdullah Al si'idi) wanda aka haifa a garin'' Unaiza '' a garin Kasim na yankin Najd da ke kasar Saudiyya. kuma mahaifansa sun rasu tun yana dan karami sai dai Allah Ya ba shi kwakwalwa da kaifin fahimta da kuma kwadayin neman ilimi. Kuma ya fara haddar Al'qur'ani da wuri har ya kamala haddar sa da kwarewa wajen karatu yana dan shekara goma sha biyu, sai kuma ya fara neman ilimi a bangarori daban daban wajen malaman garinsu da kuma wasunsu, ya bada himma ya sa kokari har ya tara ilimi mai dumbin yawa daga fannoni da na ilimai.

Kuma yana shekara 23 ya fara hadawa tsakanin neman Ilimi da kuma koyar da shi ya amfana kuma ya amfanar, ya cigaba da hakan tsahon rayuwar sa, mutane da yawan gaske sun koyi ilimi a gurinsa kuma sun amfana da shi.

Daga cikin malaman sa akwai: Shaikh Ibrahim Bn Muhammad Bn Jasir, shi ne farkon wanda yayi karatu a wurinsa . Shaikh Salih Bn Usman Alkalin Unaiza shima ya karbi Ilimin Usul, da Fiqhu, da Tauhidi, da Tafsiri,da kuma Larabci kuma ya zauna da shi har mutuwar sa ,malamin yakasance yana da mutukar sani a Fiqihu da Usulul fiqh ga kwarewa cikakkiya a Tauhidi da abinda ya dangance shi saboda shagaltuwar sa da himmatuwar sa da littattafan Ibn Taimiyya da Ibnul Qayyim. Kamar yadda ya kasance ya bada kulawa da ta wuce kowacce aTafsiri da fannoninsa har yai fice a cikin sa ya wallafa littattafai akan Tafsiri : TAISIRUL KARIMURRAHMAN FI TAFSIRI KALAMIL MANNAN yana da mujalladai takwas. TAISIR A-LADIFUL MANNAN FI KHULASATI TAFSIRIL QUR'AN. AL QAWA'ID AL-HISAN LI TAFSIRIL QUR'AN. Daga cikin littattafansa da ya kamata a mallake su da kuma fa'idantuwa da su banda wadan da suka gabata:

1- AL IRSHAD ILA MA'ARIFAT AL-AHKAM.

2- ARRIYADH ANNADHIRA

3- BAHJATU QULUBIL ABRAR

4- MANHAJ AL-SALIKIN WA TAUDHIH AL- FIQH FIDDEEN

5- HUKUMU SHURBAL-DUKKHAN WA BAI'IHI WA SHIRA'IH

6- AL 'FATWA AS SI'ADIYYA

Yana da Diwani uku na Hudubobin Mimbari, masu Amfani AL'HAKKUL WADHIH AL MUBEEN BI SHARHI TAUHIDUL ANBIYA'I WAL MURSALIN TAUDHIH AL KAFIYA AS SHAFIYA(NUNIYA IBN AL-QAYYIM).

kuma yana da littattafai da yawa a Fiqhu, da Tauhidi da Hadisi da Usul da bincke masu yawa kan ilimin, zamantakewa da fatawoyi daban daban.

Mutuwar sa: ya kamu da rashin lafiya mai tsanani farat daya ya kusanta ajalinsa kuma ya rasu daren Alhamis Ashirin da uku ga watan Jimada Thani shekara ta 1376 Hijira a garin Unaiza ya bar tabo da bakin ciki mai zurfi a zuciyar duk wanda ya san shi ko ya ji shi ko ya karanta wani abu daga gare shi, Allah Ya yi masa rahama, Ya kuma amfanar damu da Iliminsa da littattafan sa. Ameen

## GATARWAR MAWALLAFIN

Godiya ta tabbata Allah wanda Shine Ya cancanci baki dayan godiya, kuma ina shaida babu abin bautawa bisa cancanta sai Shi kadai ba Shi da abokin tarayya, kuma ina mai shaidawa Annabi Muhammadu bawan Sa ne kuma manzon Sa ne, tsira da Amincin Allah su kara tabbata a gare shi tare da alayanSa da Sahabban Sa kuma ka amintar da su.

Bayan haka: Hakika hutun zuciya, da farinciki da yayewar bakin ciki da bacin rai shi ne abin nema ga kowa da shi ne za a cimma rayuwa mai kyau kuma ya cika da farinciki da annushuwa dan cimma wadannan akwai dalilai naaddini da na al'ada wasu kuma ba za su samu ba sai ta hanyar aiki, kuma wadan nan ba za su hadu gaba daya ba sai ga muminai,

Amma wasun su koda kuma sun hada su ta wata fuskar da kokarin wasu masu hankali daga cikin su za su kufce musu ta wata fuskar mafi amfani da tabbacikuma mafi kyawun hali da kuma makoma.

Amma kuma ni a cikin wannan littafin nawa zan fadi wasu abubuwan da suka zo mun don wannan bukata madaukakiya wanda kowa yake kokarin nemanta.

Daga cikin su akwai da yawa da suka da ce da samun ta, sai suka rayu rayuwa mai dadi, wasu kuma suka rasa su gaba daya sai suka rayu rayuwa matsananciyar rayuwa mai wahala.

Daga cikinsu akwai tsaka-tsaki gwargwadon abinda aka datar da shi

Kuma Allah Shine Mai datarwa kuma Mai taimakawa kan dukkan alheri mai ijewa daga dukkan sharri.

## FASALI
## Mafi girman dalilai da kuma asalinsu da tushensu su ne imani da kuma aiki nagari.

Kuma mafi girman dalilai da kuma asalinsu da tushensu su ne imani da kuma aiki nagari

Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٧﴾ [النحل: ٩٧]

{Wanda ya aikata aiki na ƙwarai daga namiji kõ kuwa mace, alhãli yanã mũmini, to, haƙĩƙa Munã rãyar da shi, rãyuwa mai dãɗi. Kuma haƙĩƙa Munã sãkã musu lãdarsu da mafi kyãwun abin da suka kasance sunã aikatãwa.} [Surat Anahl : 97]

Allah Ya bada labari ya kuma yi alkawari ga duk wanda ya hada imani da kuma yin aiki nagari zai bashi rayuwa mai dadi a wannan gidan na duniya ,da sakamako mai kyau a wanan gida, da kuma gida matabbaci.

Dalili kan haka a bayyane yake: Hakika cewa muminai da su ka yi imani da Allah imani ingantacce, wanda yake jawuwa zuwa ga aiki nagari mai gyara zuciya da dabi'u yake gyara duniya da kuma lahira ,tare da su akwai asali da tushe da suke karbar duk wani abinda zai kaisu ga samun farin ciki da annushuwa ko kuma sababan damuwa, bakinciki da bacin rai.

Suna karbar abin da suke so, da wanda ya faranta musu, su gode da samunsu, suyi amfani da shi cikin abinda zai amfanar, idan kuma suka yi amfani da shi ta wannan hanyar sai ya samar musu da farin

ciki da nutsuwa da albarka, da fata da sakamakon masu godiya, al'amura ma su girma saboda dace da alkhairanta da albarkatunta sai su haifar da wannan farin cikin wanda shine yayansu.

Suna karbar abubuwan kida masu cutarwa da na bakin ciki da bacin rai wajen karfa abinda za su iya karfafawa ,ko kuma saukaka na saukakawa su kuma yi hakuri mai kyau kan abinda bas u da karfi akan shi ,da wannan juriyar kan abinda suke ki sai su koyi hakuri da neman lada a wajen Allah sakamakon wadannan al'amura ma su girma sai abababan kin su gushe na farinciki su maye gurbinsu da fata nagari da kwadayin samun falalar Allah - Madaukakin sarki - da kuma ladansa, kamar yadda Annabi - tsira da amincin Allah su kara tabbata a gare shi - ya bayyana a wannan hadisin ingantacce kamar yadda ya ke cewa:

"Lamarin mumini da ban mamaki yake, dukkannin al'amurransa alheri ne ,idan abin farinciki ne ya same shi sai ya godewa Allah sai ya zamar masa alheri ,idan kuma na sharri ne ya same shi sai ya yi hakuri, shi ma sai ya zamar masa alheri, sai dai hakan baya kasancewa ga kowa sai ga mumini".

Muslim ne ya rawaito shi.

Annabi - sallallahu alaihi wa sallam - ya ba da labari cewa lallai alkhairan mumini, da ganimomi da sakamakon kyawawan ayyukansa suna rubanyuwa a kowanne hali ya sami kansa na farin ciki ko na bakin ciki .

Don haka zaka ga mutane biyu wani abu na alheri ko na sharri ya same su, sai a sami banbanci ta yadda kowannen su zai karbi abin,hakan ya faru ne saboda banbancin da ke tsakanin sua fagenImani da kuma ayyuka na kwarai.

Wanda ya siffantu da wadan nan siffofi guda biyu, zaka samu ya karbi alheri ko sharri da abin da muka ambata na godiya da hakuri da abinda ya biyo bayan su, sai ya samar masa da farin ciki da annushuwa, da yayewar bakin ciki, da bacin rai, da damuwa, da kuncin rai da kuma wahalar rayuwa sai ya samu cikakkiyar rayuwa daddada a wannan gida na duniya.

Yayin da dayan yana karbar abinda yayi masa dadi, sai ya dau girman kai da dagawa, sai halayensa su canja ya juya ya koma tamkar dabba wajen hadama da tsoro, tare da haka bashi da hutun zuciya sai ma rarrabuwa ta fuska daban daban, ta fuskar tsoron gushewar abubuwan da yake so ko abubuwan da suke bijiro mai ta dalilin wadannan abubuwan, ta wani bangaren kuma ran ta kasa tsayawa kan abu daya sai dai kullum cikin shaukin wasu abubuwan daban-daban, zai cimma su ko ba zai cimmu suba, ko da ya cimma su zai dai kasance cikin damuwa ta fuskoki mabanbanta da aka ambata.

kuma yana karbar abubuwan ki da damuwa da karaya da gajiyawa kar ma a tambayi halin da ya shiga na wahalhalun rayuwa da cututtuka na tunani da fargaba, da kuma tsoro wanda zai iya kaishi zuwa ga mafi munin hali da mafi tashin hankalin damuwa, sabida baya sa ran samun wani lada ko hakuri da yake da shi da zai dauke masa kewa ya saukaka masa damuwarsa.

Dukkanin wadannan bayanan sai da aka gwada su, misali daya daga cikin wannan nau'in idan ka yi nazarin sa ka auna shi da halayen mutane, zaka ga matukar bambanci tsakanin muminin da yake aiki da imanin sa da kuma wanda ba haka yake ba, saboda addini ya na kwadaitarwa matukar kwadaitarwa kan wadatar zuci

kanabinda Allah Ya azurta bayinSa da abinda Yaba sun a daga falalarSa da karamcinSa nau'ika daban daban.

To kaga shi mumini idan aka jarabce shi da wata rashin lafiya ko talauci, ko wani abu makamancin haka wadanda ka iya samun kowa sai ka same shi da imanin sa da wadatar zucin sa da kuma yarda kan duk abinda Allah Ya tsaga masa sai ka same shi cikin farin ciki, ba zai dora wa ransa abinda ya fi karfin sa ba, yana duba ne zuwa ga na kasansa bay a duba na sama dashi da yawa ma sai ka same shi cikin farin ciki da annashuwa fiye da wanda Allah Ya bawa duk wani abu da yake bukata na duniya amma kuma bas hi da wadatar zuci .

Kamar yadda zaka sami wanda baya aiki da abinda imani yake koyarwa, ,idan aka jarabce shi da wani abu na talauci ko rasa wani abu da yake bukata na duniya sai ka same shi cikin matukar tashin hankali da tabewa.

kuma wani misalin daban: Idan dalilan tsoro, da fargaba ko tashin hankali ya mamaye shi zaka sami imani ingantacce tabbatacce a cikin zuciyarsa, mai nutsuwar ruhiya na da ikon juya shi da saukaka wannan al'amari da abinda aka hore masa na tunani da magana da aiki, ya kawar da wannan fargabar daga kansa, wadannnan halayen suna hutar da mutum kuma su tabbatar da zuciyar sa .

Kamar yadda zaka sami wanda ya rasa imani da akasin wadannan halayen idan abin tsoro ya faru da shi sai zuciyar sa ta firgita hankalinsa ya tashi, tunaninsa ya tarwatsu, tsoro ya cika shi ciki da waje da damuwa da ba zata misaltu ba.

Wannan nau'in na mutane in basu samu wasu dalilai da za suke bukata wadan da zasu gogar da su da yawa, sai su karaya su fada cikin Zulumi duka wannan saboda rasa ingantaccen Imani wanda yake cike da koyarda hakuri musamman a halin bakin ciki da firgici.

Mutumin kirki da kuma fajiri, mumini da kafiri dukkanin su suna tarayya wajen koyon jarumta da halayyar da zata saukaka musu duk wani abinda suke tsoro ko ya saukaka mu su ,sai dai mumini zai fita daban ta karfin imaninsa da hakurinsa da tawakkalinsa da dogaronsa da Allah da neman ladawasu al'amura ne da za su kara masa jarumta su kuma saukaka masa tsoron shi ta saukaka masa wahalhalu ,kamar yadda Allah - subhanahu wa ta'ala - Yake cewa:

﴿وَلَا تَهِنُوا۟ فِى ٱبْتِغَآءِ ٱلْقَوْمِ ۖ إِن تَكُونُوا۟ تَأْلَمُونَ فَإِنَّهُمْ يَأْلَمُونَ كَمَا تَأْلَمُونَ ۖ وَتَرْجُونَ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا يَرْجُونَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا﴿١٠٤﴾﴾ [النساء: ١٠٤]

{In kun kasance kuna jin radadi hakika suma suna ji kamar yadda kuke ji kuma kuna neman abinda basa saran samun sa a wajen Allah} [AL-NISA' : 104]

Kuma za su sami taimakon Allah da kusanci na musamman wanda zai tarwatsa duk wani abinda suke tsoro,

kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿... وَٱصْبِرُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ﴿٤٦﴾﴾ [الأنفال: ٤٦]

{Ku yi hakuri hakika Allah yana tare da masu hakuri} [AL -ANFAL : 46].

Kuma yana daga cikin dalilan da suke gusar da bacin rai, bakin ciki da damuwa: kyautatawa mutane ta magana da kuma aiki, da nau’o’in kyawawan ayyuka.

Dukkannin su alheri ne da kyautatawa, da su ne Allah Yake bada kariya ga mai biyayyagare shi ko fajiri daga bakin ciki da bacin rai gwargwadon kyautatawarsu ga bayin Allah, sai dai mumini ladan sa da rabonsa ya fi saboda shi kyautatawar sa saboda Allah yake yi kuma akan ikhlasi da neman lada a wajen Allah - Madaukakin sarki -, Allah Yana cewa:

﴿۞ لَّا خَيۡرَ فِي كَثِيرٖ مِّن نَّجۡوَىٰهُمۡ إِلَّا مَنۡ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ أَوۡ مَعۡرُوفٍ أَوۡ إِصۡلَٰحِۭ بَيۡنَ ٱلنَّاسِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ فَسَوۡفَ نُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمٗا ١١٤﴾ [النساء: ١١٤]

{Bãbu wani alhẽri a cikin mãsu yawa daga gãnawarsu fãce wanda ya yi umurni da wata sadaka kõ kuwa wani alhẽri kõ kuwa gyãra a tsakãnin mutãne. Wanda ya aikata haka dõmin nẽman yardõdin Allah to zã Mu bã shi lãda mai girma.} [AL-NISA’:114].

Allah Ya bada labari cewa duka wadannan al’amuran alheri ne daga inda suka fito, alkairi shi yake jawo alkhairi, yake bada kariya daga sharri, sannan cewa mumini mai neman lada Allah Zai masa sakamako mai girma a jumlace daga cikin wannan ladan mai girma :

Shi ne gushewar bakin ciki da bacin rai da gurbacewar rayuwa da mai kama da su.

## FASALI

## Cikin abubuwan da suke bada kariya daga damuwa mai tasowa da tashin hankali da shagaltuwar zuciya da gurbatattun abubuwa.

Kuma daga cikin dalilan sa suke bada kariya daga damuwa mai tasowa da tashin hankali da shagaltuwar zuciya da gurbatattun abubuwa:

Shagaltuwa da wani aiki daga aiyuka ko wani ilimi mai amfani daga cikin ilmai, hakan zai dauke hankalinsa da shagaltuwa da abinda ya dame shi, ta yuwu ma ya mantar shi gaba daya dalilan da jefa shi cikin bakin ciki sai ya samu farin ciki, nishadinsa ya karu, wannan sababin mumini da wanda ba mumini ba sun yi tarayya cikin sa, sai dai mumini zai banbanta da imaninsa da ikhlasinsa da neman lada a wajen Allah wajen shagaltuwar sa da neman wannan ilimin wanda yake koyonsa ko yake koyarwa, ya kuma ke aikata alherin da ya sani.

Idan ya kasance ibada ce to sai ya zama ansamu ladan ibada, in kuma ya kasance aiki ne na duniya ko al'ada ta duniya sai kyakkyawar niyya ta abokance ta ya nemi taimakon Allah tare da yin biyayya ga Allah,

Saboda haka wannan yana da babban tasiri wajen kore bakin ciki, bacin rai da kuma damuwa, da yawa daga cikin mutanen da aka jarrabce su da damuwa da lalacewar al'amura sukan gamu da cututtuka kala-kala sai wannan magani ne sadidan da zai warkar da shi.

Mantuwarsa ita ce sanadin bacin ransa da kuma damuwarsa, kuma shagaltarsa da aiki yana daga cikin ayyukansa.

Kuma ya kamata aikin da zai shagala da shi ya zamo ya dauke masa hankali ya kuma nutsu da shi kuma yake da sha’awa kansa; wannan zai sa ya kai ga abinda aka nufa ta mai amfani, Allah Shine Masani.

Daga cikin abinda yake bada kariya daga bakin ciki da damuwa:

Taruwar tunani gaba dayan sa da kuma mai da hankali akan aikin da yake gabansa na wannan ranar, ya kuma cire damuwa kan abinda zai zo nan gaba da kuma kan abinda ya wuce.

Kuma saboda wannan ne Annabi - sallallahu alaihi wa sallam - ya nemi tsari daga bakin ciki da bacin rai, bacin rai kan abinda ya wuce ba kuma su da kion dawo da shi baya ko sake riskarshi, sannan damuwa dan tsoron abinda zai farua nan gaba dan haka mutun ya tara dukkan kokarinsa wajen gyara lokacin da yake ciki da ranar da ya wayi gari acikin ta, idan zuciya ta hadu akan haka dole ne aiki ya kammala ya kuma sami saukin bakin cikin sa da damuwar sa .

Kuma Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - idan yayi addu'a da wata addu'a ko kuma yayi nuni ga al'ummarsa zuwa wata addu'a to yana kwadaitar da su ne tare da neman taimakon Allah da kokari matuka dan ganin abin da yake nema ya tabbata, kuma ya wofantu daga abinda yake neman tsari daga gare shi; saboda ita addu’a a hade take da aiki, bawa yana dagewa akan abinda zai amfane shi a duniya

da lahira, ya kuma rika rokon Allah samun nasara kan duk abinda yake buri, ya nemi taimakonSa akan hakan Annabi - tsira da aminci su kara tabbata a gare shi - yana cewa-:

''Ka kwadaitu kan abinda zai amfane ka, ka nemi taimakon Allah kada ka gajiya, idan wani abu ya same ka kada kace: Da na aikata kaza da kaza ne zaikasance, sai dai kace :Haka Allah Ya kaddara, kuma abinda Ya so shi yake aikatawa ,domin ita kalmar Danasani kofar Shaidan ta ke budewa''.

Muslim ne ya rawaito shi.

Annabi - tsira da amincin Allah su kara tabbata a gare shi - ya hada tsakanin umarni da kwadaitarwa kan abubuwa masu amfani a kowanne hali, da neman taimakon Allah, kar kuma ya bari karaya ko gajiyawa su rinjaye shi wannan shi ne kasala da lalaci, ya bayyana sallamawa kan abubuwan da suka shude, da sallamawa kan abinda Allah Ya hukunta.

Ya raba abubuwan gida biyu :

Kashin da mutum zai iya samar da shi ko wani bangare daga cikin sa ,ko ya hana faruwar sa ko ya saukaka shi ire iren wadannan wadannan bawa zai yi iya bakin kokarin sa ,ya kuma nemi taimakon ubangijinsa .

Daya kashin kuma hakan ba za ta yuwu ba, in hakan ya faru mutum ya kwantar da hankalinsa ya yarda ya kuma mika wuya, ba bu shakka duba da wannan tushen dalili ne da zai kawo masa farin ciki da yayewar bakin ciki da damuwa.

## FASALI
## A CIKIN MANYAN DALILAN DA SUKE SA MUTUM YAJI WASAI A KIRJINSA YA KUMA SAMI NUTSUWA

Kuma daga cikin manyan abubuwan da suke sakawa mutum yaji wasai a ransa sa ya kuma samu nutsuwa sune :

Yawaita ambaton Allah domin hakan yana da tasiri mai ban mamaki wajen sanyaya kirji da samun nutsuwa, da yayewar bakin ciki da damuwa , Allah Yana cewa :

﴿... أَلَا بِذِكۡرِ ٱللَّهِ تَطۡمَئِنُّ ٱلۡقُلُوبُ ٢٨﴾ [الرعد: ٢٨]

{Ku saurara da ambaton Allah zuciya take samun nutsuwa} [AR RA'AD :28]

Ambaton Allah yana da tasiri mai girma wajen cimma wannan abin nema a karan kansa, da abinda bawa zai samu na sakamako da lada saboda ambaton Allah.

Haka ma fadar ni'imomin Allah na zahiri da na boye, domin cewa sanin ta da fadarta suna yayewa bawa bakin ciki da bacin rai, bawa ya kwadaitu da godewa Allah wanda shine mafi kololuwar daraja kuma mafi daukaka ko da kuwa bawa ya kasance a halin talauci ko rashin lafiya ko waninsu daga cikin nau'o'in bala'ai..

Idan ya kwatanta tsakanin ni'imomin Allah da Yayi masa wadanda ba za su kirgu ba basu da iyaka, da abinda ya same shi wanda baya so sai ya ga cewa abababn kin ba za su hadu da ni'imomin da Allah Yayi masa ba .

Idan aka jarabci bawa da wani abin ki da musibu, sai ya bi da su da hakuri da yarda da kaddara tare da mika wuya sai musifun su saukaka a gare shi, idan bawa ya yi tunanin sakamako da ladan da kuma tunanin cewa hakurin da yardar ibada ne, sai zakin wannan sakamakon da zai samu a wajen Allah ya mantar da shi dacin hakurin sa.

Daga cikin mafiya amfanin abubuwa a wannan Wurin:

Amfani da abin da Annabi - sallallahu alaihi wa sallam - a cikin hadisi ingantacce inda yake cewa :

"Ku yi duba zuwa ga wanda yake kasa da ku kada ku yi duba zuwa wanda yake sama da ku hakan zai sa ku godewa Allah ba za ku raina ni'imominsa gareku ba".

[Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi].

To cewa lallai Idan bawa ya sanya wadannan abubuwan tsakanin idanuwan sa ya auna su, zai gani cewa hakika ya fi da yawa daga cikin bayin Allah ta bangaren lafiya da abinda yake da alaka da ita, ta bangaren arziki da abinda yake da alaka da shi duk tsananin halin kuwa da yake ciki ,sai bakin cikinsa, tashin hankalinsa, da kuma damuwarsa su gushe, farin cikinsa ya karu ganin cewa ya wuce da yawan mutane wurin dacewa da ni'imomin Allah - subhanahu wa ta'ala -.

Kuma duk lokacin da bawa ya zurfafa tunaninsa kan ni'imomin Allah - subhanahu wa ta'ala - ta zahiri da ta badini, na addini ko na duniya, sai ya gani hakika ubangijinsa Yayi masa ni'imomi masu yawa ya kuma kawar masa da sharrori masu yawa, babu shakka wannan yana kawar da bakin ciki da bacin rai, yana kuma wajabta jin dadi da kuma farin ciki.

## FASALI
## KAN DALILANDA SUKE SAMAR DA FARINCIKI DA KUMA WADAN DA KE GUSAR DA BAKIN CIKI DA DAMUWA

Daga cikin dalilan da suke samar da farin ciki su kuma gusar da bakin ciki da damuwa:

Kokari wajen gusar da dalilan da suke jawo bakin ciki da kuma cimma wadanda suke jawo farin ciki, wannan ba zai samu ba sai ya manta da abinda ya faru da shi na ki wanda ya wuce wanda bazai iya dawo da shi ba kuma bata lokacinsa wajen tunaninsu abubuwan wasa da abubuwan da ba zasu samu ba, sannan kuma cewa hakan wauta ne da hauka, yayi kokari ya yaki zuciyarsa wajen daina tunanin su ya kuma yake ta wajen damuwa kan abinda zai zo daga abubuwan da yake rayawa wadanda suka danganci talauci ko tsoro ko wanin haka na daga ababan ki wadanda yake tsoron faruwar su a rayuwarsa ta nan gaba.

Kuma ya san cewa lallai babu wanda ya san abinda zai faru a nan gaba arayuwarsa na daga alheri ko kona burin rayuwa ko na rashin dadinta, gabaki dayansu suna a hannun Allah Mabuwayi mai hikima, ba su hannun ba komai a hannun bayin Allah sai kokarin su ga sun kai ga alkhairai sun kuma kawar da abubuwan da zasu cutar da su kuma bawa ya sani idan ya daina bata lokacin sa wajen damuwa kan al'amuran da suka shafi rayuwarsa ta nan gaba, ya dogara ga Allah kan cewa shi zai dai dai ta masa komai ya kuma kwantar da hankalinsa idan ya aikata haka zai sami nutsuwar zuciya al'amuransa za su daidaita, bakin ciki da damuwarsa za su gushe.

Daga cikin abinda suka fi anfanar da mutum cikin lura da al'amuran rayuwarsa ta nan gaba.

Karanta wannan Addu'ar da annabi - sallallahu alaihi wa sallam - ya kasance yana yin ta:

" Ya Allah ka gyara min addini na wanda shi ne kashin bayan Al'amari na, Ka gyara min duniya ta wacce na ke rayuwa a cikinta, Ka kuma gyara min lahira ta wacce itace makoma ta ka sanya rayuwa ta zamo karin duk wani alheri, mutuwa kuma ta zamo hutu ce a gare ni daga dukkan wani sharri".

Muslim ne ya rawaito shi.

Haka kuma fadar sa :

''Ya Allah rahamarKa nake fata kar Ka bar ni da kaina daidai da kiftawar ido, ka gyaramin al'amura na ba bu wani abin bautawa da gaskiya sai kai".

[Abu Dawud ne ya rawaito shi da Isnadi ingantacce].

Idan bawa ya mai da hankali kan wannan addu'a wacce take kunshe da gyaran rayuwarsa ta nan gaba ta bangaren addini da kuma duniya da kyakkyawar niyya tare da kokarinsa wajen tabbatar da hakan Allah Zai tabbatar masa da abinda ya roka ya kuma ke fata ya kuma yi aiki domin sa, sai Ya juyar da bakin cikinsa zuwa farin ciki.

## FASALI
## CIKIN MAFI AMFANIN ABUBUWAN DA SUKE GUSAR DA DAMUWA DA BAKIN CIKI IDAN BAWA YA TSINCI KANSA ACIKIN MASIFU

Daga cikin abubuwan da suke gusar da damuwa da bakin ciki idan bawa ya tsinci kansa cikin masifu:

Ya yi kokari matuka ya ga ya saukaka su ya kuma guji duk wani sakaci da zai sake komawa cikin ta ya kwantar da hankalinsa yayi kokarin saukaka abinda zai iya saukakawa gwargwadon yadda zai iya yin hakan zai yaye masa bacin rai da bakin ciki ya tsinci kanshi cikin sabanin haka:

Kokari wajen samar da abu mai amfani da kawar da mai cutarwa gwargwadon yadda bawa zai iya.

Idan abubuwan da suke haifar da tsoro da cututtuka suka same shi, ko abubuwan da suke jawo talauci ko rashin abubuwan da yake so daga cikin ire-iren abubuwan da yake so, ya tari wadannan abubuwa cikin nutsuwa da kwanciyar hankali, kai ma wannan kwantar da ransa da yayi da juriya wajen daukar wadannan abubuwan na ki sai ya saukaka masa ya kuma gusar masa da bakin cikinta.

Musamman idan ya shagaltar da kansa kan abubuwan da zasu ba shi kariya gwargwadon ikonsa, sai ya hada kwantar da rai kokari kan abubuwa masu amfani dan

kore wadannan abin kin, tare da dogaro da Allah - Madaukakin sarki - da kuma kyautata yardarSa da shi.

Babu shakka wadan nan abubuwa suna da fa'ida mai girma wajen kaiwa ga farin ciki da walwala, tare da haka bawa yana burin samun lada da sakamako a wajen Allah - subhanahu wa ta'ala - a nan kusa a duniya ko a jinkirta masa a lahira, wannan abun mujarrabi ne kuma da yawa sun jarraba shi sun ga alherin sa matuka.

## FASALI

## CIKIN MANYA–MANYAN ABUBUWAN DA SUKE WARKAR DA CUTUTTUKAN ZUCIYA DA CUTUTTUKA NA JIKI

Kuma daga cikin manya manyan abubuwan da suke warkar da cututtukan zuciya kai har ma da na gangar jiki sune kamar haka :

Karfin zuciya, da gudun sake-sake mara sa kyau, mika wuya ga dimuwa da sake sakin rai, da za su ja mutum zuwa ga munanan tunane-tunane, saboda mutum duk lokacin da ya sallama kansa ga sake-saken zuci kamar :

Daga abinda ya shafi tsoron cututtuka da sauransu da fushi da sake -sake kan abubuwa masu radadi da fargabar faruwar al'amura mara sa kyau, da gushewar ababan so hakan sai ya jefa mutum cikin bacin rai, bakin ciki da cututtukan zuciya da na gangar jiki da cudewar al'amura wanda yana da tasiri mummuna mutane da yawa sun shaida cutarwar hakan.

Kuma ko yaushe zuciya ta dogara da Allah ta rabu da mika wuya ga munanan sake sakenta yarda da Allah tare da kwadayin falalarSa, wannan shine zai kare shi daga bacin rai da damuwa, ya kuma gusar masa da cututtukan zuci da na jiki, zuciya ta sami karfin farin ciki ya samu wanda ba za'a iya bayyana shi ba. Nawa ne asibitocin da suka cika saboda irin wadannan cututtukan da tunane-tunane suke kawowa:

Kuma da yawa wadannan abubuwan sukan yi tasiri a zuciyoyin masu karfi, banda masu rauni; nawa ne suka jefa su

cikin hauka da sakarci! mai lafiya shine kawai wanda Allah Ya kubutar da shi Ya datar dashi da kokari dan cimma abubuwa masu amfani masu karfafa zuciya, masu bada kariya daga damuwa, Allah - Madaukakin Sarki - Yana cewa :

﴿... وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسْبُهُۥٓ ...﴾ [الطلاق: ٣]

{Wanda duk ya dogara ga Allah Shi kuma Zai isar masa } [AL- DALAQ :3]

Ai Zai isar masa gaba dayan abinda yake damunsa na duniya da na lahira.

To wanda ya dogara ga Allah Shine mai karfin zuciya wanda sake-sake ba masa tasiri, sannan abubuwa basa firgita shi saboda sanin sa da cewa hakan raunin zuciya ne da ragwanta da tsoro mara sa tabbaci, a tare da hakan ya sani Allah Yana isar wa duk wanda ya dogara da shi isarwa cikakkiya, ya dogara ga Allah yayi imani da alkawarinSa, sai bakincikin sa da damuwarsa su gushe, tsananin da yake ciki ya juye ya zamo sauki, bakin cikinsa ya zamo farin ciki, tsoronsa ya koma aminci,

Muna rokon Allah ta'ala kariya, Ya azurta mu da karfin zuciya da tawakkali tabbatacce cikakke wanda Allah Yake isarwa masu shi da dukkanin alheri, ya kuma kiyaye shi daga duk wani abin ki da cutarwa.

## FASALI

## A CIKIN FADIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAM

## ''KADA WANI MUMUNI YA TSANI WATA MUMINA ''

A wata fadar kuma yana cewa:

''Fa'idodi guda biyu masu girma:

FA'IDA TA FARKO:

Kada wani mumini ya ki wata mumina in ya ki daga gareta wata dabi'ar zai so daga gare ta wata dabi'ar".

Muslim ne ya rawaito shi

Shiryarwa kan yadda zaka mu'amalanci matarka, dan uwanka, abokinka, abokin aikinka da duk wani wanda kake da wata alaka da shi ko cudanya, kuma ya kamata kasawa ranka cewa dole ne wannan din ya zamo yana da aibi ko wata tawaya ko wani abu da kake ki; idan ka sami haka sai ka hada da abinda ya kamata ka rika yi na karfafa alaka da kuma wanda zai wanzar da soyayya, wajen tuna abinda yake da shi na kyawawan dabi'u da manufofi kebantattu da sauran mutane.

Kuma da irin wannan kau da kai din ne ga barin munanawa da lura da kyawawan abubuwa na mutum, alaka da abokanta ka suke dauwama, kasamu kwanciyar hankali da hutu.

FA'IDA TA BIYU:

Itace gusar da bakin ciki da damuwa da kuma firgici da wanzuwar tsarkin rai, haka kuma da tsayuwa kan hakkoki na wajibi da Mustahabai da kuma samun nutsuwa tsakanin

bangarori guda biyu wanda duk bai shiryu da wadannan abubuwan da annabi - sallallahu alaihi wa sallama - ya ambata ba, sai akasin hakan da lura da munanan yana lura da muna nan aikin mutum ya rufe idanuwan shi daga munana, ba makawa sai ya shiga cikin damuwa babu makawa sai alakar da ke tsakaninsu da soyaya ta gurbace, kuma da yawa daga cikin hakkokin da ke rataye a wuyan su sai sun yanke su ya zamo basa kula da su.

Da yawa daga cikin mutane wadanda bakinciki mai tsanani ya same su ,musifu da tashin hankali suka afka musu suna suna hakuri da juriya su kuma kwantar da hankulansu ,sai dai kan abinda bai kai ya kawo ba sai su shiga damuwa su gurbata kyakkyawar alaka.

Dalilin da ke kawo hakan kuwa shine sun shirya wa kawunansu tarbar manyan abubuwa amma basu shirya karbar kananan ba sai su cutar da su suyi tasiri akansu, tsayayyen mutum shine a kullum yake shiri wajen tarbar manya da kananan abubuwa ya kuma roki Allah Yataimake shi akan su, kar ya bar shi da kansa dai dai da kiftawar ido to a wannan yanayin sai kananan abubuwan su saukaka a gareshi kamar yadda manyan suka saukaka a gare shi, ya wanzu yana mai samun nutsuwar zuciya da ruhi ya kuma sami hutu.

## FASALI
## KAN MAI HANKALI SHINE WANDA YA SAN CEWA RAYUWA INGANTACCIYA RAYUWA TA JIN DADI DA NUTSUWA TAKAITACCIYA CE MATUKA

Mai hankakali shine wanda ya san cewa ingantacciyar rayuwarsa rayuwar jin dadi da nutsuwa, hakika takaitacciya ce matuka bai kamata a gare shi baya karar da ita wajen bacin rai da bakin ciki saboda wannan kishiyar ingantacciyar rayuwa ce ta yaya zai bar rayuwar shi ta kare cikin haka, babu banbanci tsakanin mai biyayya da fajiri sai dai mumini yana da tabbacin wannan rabo mai yawa, da lada mai amfani anan kusa ko a jinkirta masa.

Ya kamata a gare shi idan abin ki ya same shi ko na tsoro ya hada tsakanin ni'imomin da Allah Yayi masa na addini ko wadanda suka shafi duniya da abinda ya same shin a rashin jin dadi wannan gwajin shi zai bayyana ni'imomin da yake ciki masu yawa sun ninka abinda ya same shi naki .

Haka nan kuma ya auna tsakanin abinda yake tsoron cutarwar shi da yuwuwar rashin afkuwarsu kar ya bar kokwanton afkuwar wadannan kananan abubuwan su rinjayi masu yawan .

Da wannan ne bakin cikin sa da tsoronsa za su gushe, ya kaddara cewa duk abinda zai iya yuwuwa yasame shi ya kwantar da hankalin shi idan hakan ta faru ya kuma yi kokari wajen kiyaye abinda bai faru baya kawar da wanda zai iya kawarwa ko ya saukaka shi.

Daga cikin al'amura masu amfani :

Ka sani cewa cutarwar mutane gare ka musamman ta bangaren munanan maganganunsu, ba za su cutar da kai ba, sai dai ta cutar da su, sai dai in ka shagaltar da kanka wajen

mai da hankalinka kansu ka sanya su cikin ranka, a wannan lokacin sai su cutar da kai kamar yadda ta cutar da su, idan kuwa baka kula da su ba ba za su cutar da kai da komai ba .

Ka sani cewa rayuwarka tana tafiya ne dai dai da tunaninka, in ya kasance tunaninka yakasance mai nisai ya kawo maka amfani a addininka da rayuwarka ta duniya, rayuwarka ta zamo mai kyau mai kunshe da farin ciki, in ko ba haka ba al'amarin sai ya kasance akasin haka.

Daga abubuwa masu amfani wajen kore bakin ciki:

Ka koyawa kanka cewa kada ka nemi godiya a wajen kowa sai a wajen Allah, idan ka kyautatawa wanda yake da hakki akanka ko wanda bashi da shi ka sani cewa wannan mu'amala ce tsakaninka da Alllah, kada ka damu da godiyar wanda ka kyautatawa kamar yadda Allah - Madaukakin sarki -Yake cewa dangane da hakkin bayinSa na musamman:

﴿إِنَّمَا نُطۡعِمُكُمۡ لِوَجۡهِ ٱللَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمۡ جَزَآءٗ وَلَا شُكُورًا٩﴾ [الإنسان: ٩]

{Munã ciyar da ku ne dõmin nẽman yardar Allah kawai, bã mu nufin sãmun wani sakamako daga gare ku, kuma bãmu bukatar gõdiya.} [SURATUL INSAN :9].

kuma hakan ya fi karfafa a mu'amalarka da iyalanka da 'ya'yanka da duk wanda kuke da alaka mai karfi a tsakaninku, yaushe zaka hutar da ranka ka kawar musu da sharri ka huta su ma su huta.

Daga cikin abubuwan dake kawo hutun rai, shine riko da ayyuka masu falala tare da aiki da su gwargwadon yadda ranka ya ke karkata, ba tare da ka dorawa kanka abinda zai dame ka ba, ka komo daga baya cikin kaskanci saboda baka samu wata falala

ba, saboda bin karkatacciyar hanya wacce ba ta dace ba yana daga cikin hikima mutum ya riki daukar abubuwa masu wahala ya zabi wadanda suka fi tsarki, kuma masu kyau wanda hakan zai kara masa tsarkin kai, kuma wahalhalun za su gushe.

Ka sanya al'amura masu amfani a gabanka kayi aiki dan tabbatar da su, kada ka waiwayi abubuwa masu cutarwa saboda kar su jawo maka bacin rai da damuwa ka tara hankalinka wuri guda wajen yin ayyuka masu muhimmanci.

Daga cikin abubuwa masu amfani:

Mutum ya rika yankewa da gama ayyuka kan lokaci sannan ya saurari mai zai zo a gaba; saboda ayyuka idan ba'a kare su ba sai su tarar maka wadanda suka wuce su hadu da wadanda suka zo sai su cakude maka, amma idan kayi komai akan lokaci sai ka fuskanci masu zuwa da karfin tunani da karfin aiki.

Ya kamata ka zabi ayyuka masu muhimmanci masu amfani, sannan a cikin masu muhimmancin ma ka zabi wadanda suka fi, ka maida hankalinka kansu kan wadanda kafi karkata gare su, kuma wadanda kafi sha'awa domin cewa akasin hakan yakan haifar da gajiyawa tare da tabarbarewa, ka nemi taimako kan haka ta yin kyakkyawan tunani tare da neman shawara, saboda duk me neman shawara baya yin da na sani ka nazarin abinda ka ke son aikatawa tunani mai kyau idan ka tabbatar da masalahar saka yi azama sai ka dogara ga Allah, hakika Allah Yana son masu tawakkali.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su kara tabbata ga Annabi Muhammad da alayansa da sahabban sa.

## Abubuwan da ke ciki

TAKAITACCEN TARIHIN MAWALLAFIN WANNAN LITTAFIN .........3

GATARWAR MAWALLAFIN .........6

FASALI MAFI GIRMAN DALILAI DA KUMA ASALINSU DA TUSHENSU SU NE IMANI DA KUMA AIKI NAGARI. .........7

FASALI CIKIN ABUBUWAN DA SUKE BADA KARIYA DAGA DAMUWA MAI TASOWA DA TASHIN HANKALI DA SHAGALTUWAR ZUCIYA DA GURBATATTUN ABUBUWA. .........13

FASALI A CIKIN MANYAN DALILAN DA SUKE SA MUTUM YAJI WASAI A KIRJINSA YA KUMA SAMI NUTSUWA .........16

FASALI KAN DALILANDA SUKE SAMAR DA FARINCIKI DA KUMA WADAN DA KE GUSAR DA BAKIN CIKI DA DAMUWA...18

FASALI CIKIN MAFI AMFANIN ABUBUWAN DA SUKE GUSAR DA DAMUWA DA BAKIN CIKI IDAN BAWA YA TSINCI KANSA ACIKIN MASIFU .........20

FASALI CIKIN MANYA–MANYAN ABUBUWAN DA SUKE WARKAR DA CUTUTTUKAN ZUCIYA DA CUTUTTUKA NA JIKI .........22

FASALI A CIKIN FADIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAM ‘’KADA WANI MUMUNI YA TSANI WATA MUMINA ‘’ 24

FASALI KAN MAI HANKALI SHINE WANDA YA SAN CEWA RAYUWA INGANTACCIYA RAYUWA TA JIN DADI DA NUTSUWA TAKAITACCIYA CE MATUKA .........26

ABUBUWAN DA KE CIKI .........29

رئاسة الشؤون الدينية بالمسجد الحرام والمسجد النبوي